# MAGAMA

Mayu/Yuni 2006 Rabi'ul Akhir Jimada Ula 1427 Kyauta



## Mayar Da Aikin Sa Kai Halin Rayuwa Na Da Muhimmanci

ISSN 0794-0262

# Yarjejeniyar Zaman Lafiya A Darfur



An daɗe ana ja, amma daga ƙarshe ƙwalliya ta biya kuɗin sabulu



Muƙaddashin Sakatariyar Harkokin Wajen Amirka Robert Zoelick (a hagu) tare da Wakilin Tarayyar Afirka Salim Ahmed Salim (a dama)



Wakilim Gwamnatin Sudan Magthoub el Khalifa (a dama tare da Shugaban ƙungiyar sojin 'yantar da Kudancin Sudan mafi rinjaye a ƙasa, Minni Minnawi a lokacin da yake sa hannu a yarjejeniyar sulhu



Shugaban tawagar Gwamnatin Amirka, Mista Robert Zoelick a lokacin da yake zantawa da Shugaba Obasanjo



Mai Masaukin baki a taron sulhunta ɓangarorin da ke 'yaƙi a Darfur, Cif Obasanjo yana musabaha da wakilin Gwamnatin Sudan Magthoub el Khalifa



Shugaba Obasanjo tare da Shugaban sojin da ke 'yaƙin yantar da Kundacin Sudan mafi rinjaye, Minni Minnawi

MAGAMA

Mayu/Yuni 2006 Rabi'ul Akhir/Jimada Ula 1427 Kundi Na 1, Fitowa Ta 23



Claudia E. Anyaso

Wannan lokaci ne na maraba da kuma bankwana. Da yawa daga cikin jami'an difulomasiyya, haɗe har da ni muna dab da kammala adadin lokacin aikinmu a Nijeriya, kazalika wasu za su maye gurbinmu. Mu da ke a sashen hulɗa da jama'a na da kyakkyawan sa'an aiki. Zan koma gida a Washington a inda zan karɓi aikin Darakta, a ofishin da ke ƙula da harkokin difulomasiyya da hulɗa da jama'a a Sashen kula da Nahiyar Afirka na Ma'aikatar Harkokin Waje. Wannan ofishin ne yake kula da harkokin difulomasiyyarmu da Nijeriya da kuma sauran ƙasashe 37 a Nahiyar Afirka. Na ɗauki kaina tamkar mai babban sa'a, domin samun dama da na yi na ci gaba da aikin da na saba da shi.

Magajiyata a matsayin Babbar Jami'ar Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya ita ce Mis Atim George wacce shekara uku ke nan take kula da wannan fanni a ƙaramin ofishin jakadancinmu da ke birnin Legas, kuma idan za ku tuna, ita ce ke gabatar da mujallunmu na CROSSROADS da MAGAMA a wasu lokutan. Ta san Nijeriya da al'adunta sosai. Tana kuma ƙoƙarin ƙarfafa danƙon zumunci da al'ummar ƙasar. Dalili ke nan da ya sa mai martaba sarkin Ife (Ooni) ya ba ta sarautar (*Yeye Araba*) bayan karrama ta da Jami'ar Babcock ta yi ta ba ta kyautar Babban digiri a kwanan nan. Na tabbata cewa za ku yi mata kyakkyawar tarba a wannan sabon matsayin da za ta gada kamar yadda kuka ba ni kyakkyawan haɗin kai da nuna mani ƙauna.

Zan kammala saƙona da tsokaci a kan harkokin dimokuraɗiyya. Gwamnatin Amirka ta jinjina ma Nijeriya da Shugaba Obasanjo da kuma jama'ar Nigeriya da ke goyon bayan dimokuraɗiyya a zaɓen 2007. Mu Amirkawa na yabon ƙoƙarin jama'ar Nijeria na kawo canji ta hanyar karɓaɓɓen tsarin dimokuraɗiyya.

Dimokuraɗiyya na bukatar tsoma baki da gwagwarmayar al'umma cikin tsarin mulkinsu kamar yadda labarin aikin sa-kai da ke cikin wannan wallafa ya nuna. Zaɓe da 'yancin faɗar ra'ayi da 'yancin 'yan jaridu suna cikin allamun halin dimokuraɗiyya mai kyau. Haka kuma, Ambasada Campbell ya yi jawabi a kan muhimmancin zaɓe. Ni kaina, ina fatan za a yi zaɓen 2007 cikin walwala da, gaskiya da, zaman lafiya da rashin tababa saboda samun ci gaban dimokuraɗiyya a Nijeriya.

## Abubuwan Da Ke Ciki

Muhimmancin Aikin Sa-Kai Ga Ranar Kyautata Muhalli Ta 2006 — 2
Ya Duƙufa Ga Inganta Yankinsa — 4
Matashiya A Aikin Sa-Kai — 5
Mene ne Aikin Sa-Kai? — 7
Hanyoyin Da Kungiyoyin Sa-Kai Ke Taimaka Wa Mutane — 7
Shugaba Bush Ya Jinjina Wa 'Yan Fito: Ku Yunƙura Don Taimakawa — 8
Nijeriya Ta Samu Agaji Don Magance Illar Tsirrai Domin Taimaka Wa Noman Fadama — 9
An Buɗe Cibiyar Amirka A Bauci — 10
"Al'umma Ɗaya Makoma Ɗaya": Saƙo Daga Amirka — 11
An "Amince Da Zaman Lafiya" A Darfur — 12

MA'AIKATAN MUJALLA

CLAUDIA E. ANYASO
Jami'ar Hulɗa Da Jama'a A Nijeriya

RUDOLPH E. STEWART
Jam'in Labarai

SANI MOHAMMED
Edita

ISHAKA ALIYU
Mai Ba Da Shawara Game Da Wallafawa

Ofishin Jakadancin Amirka ke wallafa wannan mujallar kowane wata. A aiko da wasiƙu zuwa ga Sashen Hulɗa da Jama'a, Lamba 1075 Titin Difulomasiyya, Tsakiyyar Gari, akwatin gidan waya mai lamba: 5760, Abuja, Nijeriya. 09-4614000 Fax: 09-4614011. Ofishin na Legas: akwatin gidan waya mai lamba: 554, Legas. Tel: 01-2632577, 2633560, 2633395. Na'urar INTERNET: http://nigeria.usembassy.gov/wwwhmagama.html

# Muhimmancin Aikin Sa-Kai Ga Ranar Kyautata Muhalli Ta 2006

*Daga Ibrahim Dan-Halilu*

Masu fafitikar kyautata muhalli, a duk duniya, suna murnar tunawa da yanayin Duniya ranar 22 ga watan Afrilu. A Nijeriya, Ofishin Jadakancin Amirka, tare da haɗin gwiwar fiye da ƙungiyoyin gwamnati da masu zaman kansu 12, suka shiga bikin murnar tunawa da ranar, a Babban Birnin Tarayya da kuma shuka itatuwa a harabun ofisoshin Gwamnatin Tarayya da sauransu.



Dokta Victor Fodeke na Haɗaɗɗar ƙungiyar kula da Muhalli ta Afirka (a tsakiya) tare da Matasa da suke aikin bautar ƙasa waɗanda suka taimaka wajen tsabtace birnin Abuja ta hanyar tsintan Ledojin Fiyo wota.

Maƙasudin bikin shuka itatuwan shi ne don janyo hankalin 'yan Nijeriya, musamman matasa, a kan muhimmacin shuka itatuwa a yanayin da muke ciki da kuma kwaɗaita wa masu taimakon sa-kai amfanin ayyukansu ga jama'a.

Tun ranar 20 ga watan Afrilu, Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka ya shirya wani zama na musamman da manema labarai, daga kafofi fiye da 20, game da shirin bikin.

Manyan 'yan fafitikar kyautata muhalli da suka yi jawabi a bikin na Jakadancin Amirka, a taƙaice, sun yi bayanai ne game da muhimmancin Ranar Duniya ga ɗan-Adam da kuma bukatar ƙara kula da muhalli.

Wani babban jami'in Ma'aikatar Kula da Muhalli ta Tarayya, Malam Ahmad Sanda, wanda ya taɓa halartar shirin ƙaro ilimi na duniya, ya ce ko kusa ba daidai ba ne, a bar wani mutum ko wata 'yar ƙungiyar jama'a kaɗai, su shugabanci shirin magance illolin da ke addabar jama'a kaɗai, ciki kuwa har da taɓarɓarewar muhalli.

Jawabin Malam Sanda ya ƙayatar game da dangantakar da ke tsakanin matsayin tattalin arziki da rashin kula da muhalli. Ya ƙi amincewa da wai fatara ce ke haddasa rashin kula da muhalli. Ya bayyana cewa, ba ga marasa galihu ya kamata a ɗora laifin ba, idan aka lura da yadda masu hali ke nuna halin ko-oho.

A cewar Malam Sanda babu masu laifin jibge datti da sauran ƙazantar da ke gurɓata muhalli irin masu halin rayuwar masu hannu da shuni. "Idan ka lura, da kyau, mafi yawan ƙazantar da ke addabar mu masu hannu da shuni ke haddasa ta a birane. Idan na je ƙauye, sai in ga cewa mutanen karkara sun fi mu tsabta", in ji shi.

Ɗan Majalisar Dattijai Gaylord Nelson na Winsconsin, ne ya fara jagorancin zanga-zangar ƙyamar gurɓatar muhalli, "don girgiza shugabannin siyasa da jami'an tsaro don saka wannan al'amarin a cikin harkokin ƙasa", shi ya kawo ƙirƙiro Hukumar Kare Muhalli da kafa dokar tsabtace ruwa da kare dabbobin da ba su da yawa a duniya, a Majalisar Dattijan Amirka.

Babbar galabar da aka samu ita ce, irin hukuncin da 'yan jaridu suka yanke na janyo ra'ayoyin jama'a da inganta haɗin gwiwar ƙungiyoyi, a kan al'amurran da suka shafi tsabtar muhalli. Amma ya yi tir da halayyar 'yan jaridun Amirka, wajen rashin bayyana irin illolin da gurɓatar yanayi ke kawo wa mutane, duk da yake bincike ya nuna ɗimbin

matsalolin da ake samu game da kazantar muhalli, tun cikin 1960 har ya zuwa 1970.

Lokacin da yake gabatar da jawabinsa, Dokta Victor Fodeke, na Haɗaɗɗar Kungiyar Kula da Muhalli ta Afirka, wadda ita ce ke da silar asalin kafuwar tsaida Ranar Duniya ya bayyana cewa Ranar Duniya wata baiwa ce ga Amirka da kuma duniya, domin ita ta tursasa wa Majalisar Ɗinkin Duniya yanke yarjejeniyar keɓe ranar 22 ga watan Afrilun kowace shekara don tunawa da muhalli da kunnowar hukumomin kula da muhalli, a duk duniya, da ke matsa lamba ga gwamnatoci don ƙudurorin muhalli da tilasta yin aiki da kyautata amincin kayayyaki.

Ya roƙi 'yan jaridun Nijeriya da su jagoranci gangamin tilasta wa gwamnati mayar da hankali ga kwararowar Hamada a Arewa da ɓulɓular mai da kazanta a Kudu da kuma janyo hankalin ƙungiyoyin gwamnati da masu zaman kansu, don cimma wannan manufa ta ƙoƙarin kawo canji ga abubuwan da ke cutar da 'yan-Adam.

Masana sun lura cewa yawan gurɓatar iska da ruwa, kazalika da sauran harkokin bil-Adama, su ke sa zafin yanayin da ke kawo mana waɗansu illolin da ke fin ƙarfinmu. Irin wannan yanayin yana shafar kayayyakin abinci da ruwan sha, da torokon teku da tsibirin ƙanƙara da ke kashe itatuwa da dabbobi da dama, ya kuma sa yaɗuwar cututtuka.

Don yin rigakafi, Ranar Duniya, a wannan shekarar, ta sa taken "Magance Canjin Yanayi", da nufin ilmantar da jama'a da gwamnati da kamfanoni da ƙungiyoyin gwamnati da masu zaman kansu, da neman taimakon haɗin gwiwa, don dakatar da gurɓatar da yanayi.

Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka da ƙungiyoyi 12 ne suka shirya Bikin Ranar Duniyar na bana, da nufin gabattar da Kungiyar 'E-Net Africa,' wanda aka ƙaddamar shekaru uku da suka wuce. A harkokin ilmantarwa kuma, an tattauna a Gidan Telebijin Na Kasa da ke Abuja, a kan matsalolin da gurɓacewar muhalli ke kawo mana, da kuma hanyoyin magance su.

Baƙi daga Ofishin Jakadancin Amirka da Kungiyar Kula da Muhalli ta Duniya da Babban Asibitin Kasa da ke Abuja da kuma ƙungiyoyoyin gwamnati da masu zaman kansu ne suka tattauna, inda suka zurfafa yin bayanai ga tarihi da ci gaban da aka samu game da Ranar Duniya a Nijeriya. Kowannensu ya bayar da misalai, an kuma yi masa tambayoyi daga masu bugo wayar tarho, har tsawon awa ɗaya.




Ɗaya daga cikin motocin da suka taimaka ga ɗiban 'yan aikin sa kai da suka zagaya birnin Abuja domin wayar ma jama'a kai game da amfanin tsabtace muhalli.


Aikin sa kai na bukatar taimako na ƙarfin jiki, ko kuma dukiya.

Duba Shafi Na 6

# Ya Duƙufa Ga Inganta Yankinsa

*Aikin sa-kai sai wanda ya daure. Yi wa al'umma hidima kyauta. Rayuwar Elkana Aliyu ta zama abin koyi ga ayyukan jinƙai, tun lokacin da ya sauke karatun jami'a, shekaru goma da suka wuce. Ya sadaukar da kansa ga yi wa yankinsa hidimar da jama'a da dama ke amfana a Jihar Bauci. Ga yadda labarin ya ke.*




Shugaban ƙungiyar Taimakon kai na "wurno kowa naka," Malam Elkana Aliyu tare da jami'in kula da Ɗakunan karatu na Amirka, Mista Henry Mendelsohn.

"Tun lokacin da na kammala karatun jami'a, jama'ar yankina, wanda ake kira Wurno, a kudancin Jihar Bauci, kamar kilomita 90 daga garin Bauci, suka roƙe ni da in shugabanci harkar aikin taimakon kai-da-kai da bayar da shawarwari a kan abubuwan da ke ci wa yankin tuwo a ƙwarya. Jama'ar Wurno suna yankin karkara ne, inda babu abubuwan jin daɗin rayuwa. Bayan haka, ƙoramu da koguna sun yi wa yankin zobe, inda da wuya ka je nan da can lokacin damina. Wannan shi ya sa na fara gudanar da ayyukan taimakon kai-da-kai a yankin. A wajen wani babban taron da aka yi ne, a cikin watan Janairu na 1995, aka gano dukan bukatun da wannan yanki yake da su. Bukatun sun haɗa da rashin wurin shan magani da ruwan sha da rashin hanyoyi da kuma aikin yi. Amma bukatar wurin shan magani ta ɗara kowace bukata, wannan kuma shi ya sa a matsayina na shugaban Ƙungiyar Ci Gaban Wurno Kowa Naka, sai jama'ar Wurno suka duƙufa ga ginin ɗakin shan magani. Ya zuwa 1996, gini ya yi nisa, lokacin da ƙaramar hukuma ta taimaka da buhunan siminti. Daga nan sai muka fara neman taimako ga ƙungiyoyin duniya. A cikin 1998 sai ga Naira miliyan ɗaya da dubu 400, aka kuma kammala ginin wurin shan maganin. A halin yanzu ma, wurin shan maganin ya fara aiki, kuma yana biyan bukatun jama'ar yankin.

A kuma bisa ga ƙoƙarinmu na magance matsalar ruwan sha, a yankinmu da sauran yankunan maƙwabta, mun samu tallafin dalar Amirka dubu huɗu daga Jakadan Amirka, don aikin taimakon kai-da-kai. Bugu da ƙari, a ƙarƙashin Ƙungiyar Ci Gaban Wurno Kowa Naka, mun yi amfani da wannan tallafi wajen haƙa rijiyoyin burtsatse shida a Wurno da kuma yankin maƙwabta. A 2003, mun ɓullo da



'Yammata da suka koyi sana'ar yin jikunan mata daga ƙungiyar "Wurno Kowa Naka" da ke Jihar Bauci.

# Matashiya A Aikin Sa-Kai

wani asusun ilmi, don taimaka wa iyalan daba su iya biyan kuɗin makarantar yaransu. Da wannan tallafi ne daga masu hannu da shuni, iyalai 22 daga yankunan Wurno da Bajama suka samu gurabe uku-uku kowanne, yanzu kuma suna iya biyan kuɗin makarantar yaransu tun daga firamare har jami'a.

Kwanan nan na dawo daga wani taron mako uku da Gwamnatin Amirka ta shirya, a ƙarƙashin Shirin Koyo Ilimi A Kasar Waje Don Matasa. Lokacin da na dawo kuma, na gudanar da ayyukan inganta harkokin matasa, da taimakon kai-da-kai da na sa-kai da inganta hanyoyin sanin shugabanci. Kwanan nan kuma na shirya wani taron bita ga yammata da ba su da sana'a, a mujami'armu.

Dukan waɗanda suka halarci taron bitar kuwa sun amfana da ilmin yin duwatsun wuya da 'yan kunne, wanda yanzu mata ke saye daga tsakanin dalar Amirka biyar zuwa 20. Tuni ma har waɗansu ɗaliban sun sauke. A halin yanzu ina shirin kafa wata cibiyar mata, a yankuna biyu, tare da haɗin gwiwar ƙaramar hukumar Tafawa Balewa da ke Jihar Bauci, domin aiwatar da abin da na koyo a shirin na Amirka". ■

- Bincike, ko al'amurran da ke da amfani gare ka.

Ka nemi gudunmawar jama'ar da za ku yi aiki a kan al'amurran da suka kwanta maka a zuci. Mai yiwuwa kana bai wa waɗansu ƙungiyoyi kuɗin da zai iya zama masomin da za ka fara sanin aikin sa-kai. Idan har ba ka samu wata ƙungiya ba, to, me zai hana ka fara wani abu? Kana iya kiran maƙwabtanka, don share unguwarku, ko kuma sintiri, ko fentin gidan ajiyar tsofaffi, ko lura da marasa lafiya, a kan titi, ko ku yi rundunar bayar da shawarwari a kan magance munanan ɗabi'u a tsakanin maƙwabtanku. Kai aikin sa-kai bai da iyaka, domin bukatun jama'a suna da yawa.

- Ka yi tunanin irin basirar da kake da ita.

Idan ka fi son yin aiki a waje ne, ko kana son koyarwa, ko hulɗa da jama'a, to kana da bukatar binciken wurin da za ka bayar da gudunmawar waɗannan halayen rayuwa naka. Muƙamai da dama suna bukatar wanda ke da masaniyar sarrafa waɗansu injuna, ko na'urori masu ƙwaƙwalwa, ko wanda yake da fasaha, kamar harkokin sadarwa da guje-guje. A matsayinka, kana iya yin wani abin da ya yi daidai da ayyukan da kake yi, lokacin da kake ma'aikaci, ko kake yi don shaƙatawa. Wannan muƙamin zai sa, ba tare da wata-wata ba, ka tsunduma ga yin aiki, ba tare da ka yi wata bita ba.

- Kana son ka koyi wani abu sabo?

Mai yiwuwa kana son ka koyi wata sabuwar fasaha, ko masaniya game da wani al'amari. Ka yi tunanin inda za ka shiga aikin sa-kai, domin ka koyi wani abu sabo. Misali, ka yi tunanin yi wa 'yar jaridarku, da ke yayata fa'idar kula da dabbobi, to za ka inganta masaniyarka game da aikin jarida, wadda tana iya taimakonka ga aikin da kake yi. Ko kuma aikin sa-kai na iya canja wata ɗabi'a da kake da ita. Misali, idan kai ma'aikacin ofis ne kana da ayyuka da dama da za ka yi, kamar yawon buɗe ido a wuraren ajiye kayayyakin tarihi, ko killace filin wasa. Akwai ƙungiyoyi da dama da ke bukatar horar da masu aikin sa-kai. Amma sai ka yi amannar cewa wannan aikin na bukatar sadaukar da kai, kafin ka fara.

- Tattara bukatunka wuri guda.

Nemi wuraren da ke gudanar da aikin sa-kai, wannan ne zai sa cimma biyan bukatar rayuwa. Misali, Idan kana son ka rage ƙiba, to ka fara aikin sa-kai, kamar share wuraren da jama'a ke hutawa, ko aiki a gidan tarbiyyar yara. Ko kuma idan kana da sha'awar dafa abinci ne, to je ka wurin da ake koyar da dafa abinci, don basirarka ta faɗaɗa.

- Kada ka nuna haɗama a kan abinda za ka yi.

Ka tabbatar duk lokacin da za ka keɓe don yin wani aiki, ba zai matsa maka ba, don kada iyalanka su koka, ko ka gaji, ko ka kauce wa manufar ƙungiyar da kake yi wa aiki, ko wurin aikinka. Shin kana son aiki na din-din-din ne, ko kuma na wani ɗan gajeren lokaci? Idan ba ka tabbatar ba, ko kana wasi-wasin za ka iya aikin, kafin ka duƙufa, to ka ɗan fara da ƙungiyar da ba za ta cinye maka lokaci ba, har sai ka gamsu. Kuma ka fara a hankali, maimakon ka rakito abin da ba za ka iya ba. ■

Daga Shafi Na 3

Muhimmancin wannan tattaunawa ta telebijin, ita ce a gabatar da ayyukan da ƙungiyoyi ke yi a Amirka game da wannan muhimmiyar rana da kuma yadda ƙungiyoyin Nijeriya ke koyo daga gare su, don sanin bambanci. Da wata manufa Ofishin Jakadancin Amirka ya sanya ƙungiyoyinmu na cikin gida, wajen gudanar da shirye-shirye, yayin da ofishin ya kula da yadda ake gudanarwar don samun biyan bukata.

Kungiyar E-Net Africa ce ta yi jagorancin kula da gudanar da tattaunawar har sau biyu, ta kuma samo ɗaliban jami'a 100 da ke bauta wa ƙasa, don jerawa da sauran ƙungiyoyi, wajen bikin shuka itatuwa da gangami, ranar 22 ga watan Afrilu.

Sauran ƙungiyoyin da suka shiga sahun bikin, sun haɗa da Kungiyar Kare Haɗurra da Shirin Koyon Karatun Ɗaliban Kasashe IVLP ke gudanarwa, ƙarƙashin jagorancin Mista Lawrence Olanrewaju Osho da Kungiyar Kula da Muhalli ta Nijeriya da Kamfanin ɗaukar hoto da harkokin 'yan jaridu na Eagleview Production, wanda tsohon shugaban Kungiyar ta IVLP, Mista Patrick Otoro, ke shugabanta. Akwai kuma Kungiyar Lura da Muhalli ta Duniya da kuma Kungiyar Rotary ta Asokoro.

Ita ma Kungiyar Direbobi ta Kasa ta shiga bikin, tun lokacin da aka fara bikin wannan shekara na Ranar Duniya. Ko da yake ƙungiyar ba ta shiga tsundum ba, cikin gangamin, kamar yadda aka zata, 'ya 'yanta sun yi gangami a Tashar motar Jabi. Wakilan, waɗanda mafi yawa direbobi ne da 'yan kamasho, sun yi amfani da takardun Ranar Duniyar, waɗanda Haɗaɗɗar Kungiyar Kula da Muhalli ta Afirka ta buga, inda take cewa: "A shuke Abuja a kuma raba ta da ƙazanta". Gangamin ya leƙa gidaje misalin dubu biyu a yankuna huɗu na Abuja, yayin da mutane fiye da dubu 50 suka ga tattaunawar da aka yi a gidajen telebijin na AIT da NTA.

Ita ma Ma'aikatar Muhalli ta Tarayya, wadda ta bayar da irin yaɗawa, a lokacin bikin shuka itatuwan, ta aike da mutane 15, cikinsu har da mataimakin 'director', a wajen gangamin. Mafi yawan waɗanda suka shiga gangamin sun fito ne daga ƙungiyoyin kula da muhalli da 'yan bauta wa ƙasa, kusan dubu biyu, da suka shiga aikin sa-kai. Kungiyoyin kula da muhallin sun yi ayyuka iri-iri da dama. Sun shuka itatuwa da gina gadoji da yaƙar jahilci da dai sauran ayyukan da gwamnati da ƙungiyoyi za su kashe maƙudan kuɗi.

Wani muhimmin bikin da aka shirya, don tunawa da ranar shi ne bikin baje koli da ƙungiyar Tsofoffin Ɗaliban Shirin Hubert Humphrey a Nijeriya ta gudanar. Bikin ya nuna wallafe-wallafe da kayayyakin da suka shafi muhalli da ɗaliban makarantun firamare da suka yi wasan kwaikwayo kan tsabtace muhalli. Manufar baje kolin shi ne a janyo ra'ayoyin jama'a da kamfanoni da ƙungiyoyi da gwamnatoci ga irin ƙalubalar da duniya ke fuskanta wajen kyautata muhalli.

Jerin-gwanon ya taso ne daga Kubwa, wajen ƙarfe goma na safe, ranar Asabar 22 ga watan Afrilu, tare da mutane fiye da 130 da suka yi ta leƙa tashoshin mota da kulob-kulob na Babban Birnin Tarayya, inda aka riƙa aike wa jama'a da saƙonnin taken wannan shekarar.

Bikin na bana ya nuna muhimmancin haɗin gwiwar jama'a da gwamnati wajen magance illolin gurɓacewar muhalli. Kuma irin yawan jama'ar da suka shiga bikin wata alama ce ta za a samu nasara.

Manufar masu kishin tsabtace muhalli shi ne su kafa wani kwamiti na din-din-din da zai riƙa gudanar da harkokin wayar da kan jama'a da ba su zimmar da ake bukata don kare duniya daga haɗarorin da gurɓacewar yanayi da wani saken jama'a ke cutar da bil-Adama. Kuma Ofishin Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka yana sahun gaba a wannan harkar.

Ofishin zai yi aiki da Kungiyar E-Net Africa da sauran abokan haɗin gwiwa, don shirya wani taron gwamnati da kamfanoni da ƙungiyoyi, wajen kafa turbar Kwamitin Tunawa da Ranar Duniya a Nijeriya, wanda zai riƙa fiddo da shirye-shirye da bunƙasa ayyuka, kowane lokaci, don ilmantarwa da janyo hankali da tsoma bakin duk wani mai bukata, wajen inganta harkokin kula da muhalli.

Manufa ita ce a janyo hankalin kamfanonin haƙar mai da ƙungiyoyin ƙwadago da 'yan kasuwa da shugabannin al'umma da matasa da ɗaliban sakandare. Ofishin yana fatan janyo hankalin masu ayyukan sa-kai daga dukan ɓangarorin gwamnati da kamfanoni da ƙungiyoyi masu zaman kansu, a cikin al'amarin. ■

# Mene ne Aikin Sa-Kai?

## Hanyoyin Da Kungiyoyin Sa-Kai Ke Taimaka Wa Mutane

- Gidajen Marasa Muhalli
- Wuraren Ajiyar Abinci
- Aikin Agaji na ƙungiyar Red kuros da Red Kresent
- Kungiyar Muhalli Don Taimako kan gina gidaje ta bai wa marasa galihu, a yankuna. Masu aikin sa-kai ba waɗansu kaɗai suke taimakawa ba, har ma sukan koyi yadda ake gina gidaje.
- Wuraren Shaƙatawa
- Shirye-shiryen Garuruwa
- Taimaka wa Jama'a Koyon Karatu
- Asibitoci
- Ɗakunan Ajiyar Litattafai
- Gidan Tsofaffi
- Kula Da Dabbobi
- Kungiyoyin Kyautata Muhalli
- Yaƙin Neman Zaɓe ■

Aikin sa-kai yana da wata martaba ga jama'a, wanda a wani lokacin ma akan bayyana shi da cewa yana ƙara danƙon zamantakewar kowane jinsin jama'a. Ana samun masu aikin sa-kai, a kowane jinsin jama'a, ya Allah dattijai ne, ko majiya ƙarfi, talaka ko mai hali. Kuma aikin sa-kai, shi ya fi kowane aiki tabbatar da kishin zuci da jin ƙan jama'a a ƙasashen Amirka da Kanada, hatta ma a Nijeriya. Kungiyar "Red Cross" da ta "Rotary" da ke Nijeriya da Kulob ɗin Nijeriya da Sojojin Sa-Kai da Kungiyar 'Boy Scout' da sauran ƙungiyoyin matasa, sukan sadaukar da rayuwarsu ga taimaka wa ɗan Adam.

Wannan kuma shi ne ke tabbatar da haƙƙin maƙwabtaka, ya ƙara danƙon zumuncin mazauna wuri, idan jama'a suna taimaka wa juna da inganta yanayin rayuwarsu.

Sai da bayar da gudunmawar kyautata halin rayuwar jama'a, masu ayyukan sa-kai za su rage irin wahalolin da jama'a ke shiga, yayin da za su samu ƙishin zuci bisa ga manufofinsu da kuma canja halayyar jama'a. Jama'a na ƙoƙarin inganta rayuwar jama'a, wanda daga bisani tasu ta yi kyau.

Aikin sa-kai yana haɗa kan jama'a da sanya su hulɗa da amincewa da juna. A bisa ga wani kididdiga da Hukumar Alƙaluma ta Kanada ta yi a 2000, masu aikin sa-kai da masu taimaka masu, ya zuwa watan Agustar 2001, sun shafe aƙalla awowi miliyan dubu ɗaya, suna bauta wa jama'a, wanda aikin da suka yi, an ƙiyasta shi da daidai da na ma'aikata dubu 549. Idan kuma aka danganta al'amarin da kuɗi, to wannan aikin da masu aikin sa-kan suka yi, ya tasar ma na dalar Amirka miliyan dubu 17, a shekara, idan aka kwatanta shi da awowi 40 da ma'aikaci ke yi a cikin mako guda.

Mene ne bambancin aikin sa-kai da barance?

Aikin sa-kai dai, mutum ne ke sa kansa. Ba dole ba ne, ba kuma bauta ba ce. Yana taimaka wa mutane da ɗaukacin jama'a, kuma ƙungiyoyi masu zaman kansu ne kan ɗauki ɗawainiyar shi, ba tare da sai an yi wata jinga ba. Ayyukan barance kuwa sun haɗa har da Bauta wa Kasa da waɗansu hidimomin da ake yi a makarantu, bisa ga umurnin hukuma.

Ko da yake aikin sa-kai ya yi kama da barancen, amma jama'ar da



Aikin sa kai domin tsabtace Muhalli da aka aiwatar a birnin Abuja a Shekarar 2004 tare da haɗin gwiwar ƙungiyar kare Muhalli ta Duniya.

ke sadaukar da rayuwarsu don inganta rayuwar al'ummarsu, ba su samun godiyar daya kamata a yi masu. Dole kuwa jama'a su girmama da tallafa wa masu aikin sa-kai.

Wane ne mai aikin sa-kai?

Masu aikin sa-kai kan kasance manya ko yara, dattijai ko majiya ƙarfi, talakawa ko masu hannu da shuni, da ke sadaukar da kawunansu, saboda waɗansu dalilai, don ganin jama'a sun ci gajiyar wata baiwar da Allah ya yi masu.

Ba wai don kuɗi suke yi ba, sai dai irin tukuici, ko ƙoshin zuci da godiya da kuma magance zaman banza. A ko da yaushe masu aikin sa-kai kan gano ayyuka iri-iri da tabbatar da ganin cewa jama'a sun amfana.

Ka natsu da tausayawa ga irin taimakon sa-kan da za ka yi, da kuma irin haƙilonka, wanda wannan kaɗai ya ishe ka biyan bukata. Abin da za ka samu bai da iyaka! ■

# Shugaba Bush Ya Jinjina Wa 'Yan Fito:
## *Ku Yunƙura Don Taimakawa*

Awani ɓangare na Makon Tunawa da Ma'aikatan Aikin Sa-kai, Shugaba Bush, kwanan nan, ya yi aiki da 'yan fito, a gaɓar tekun Amirka, inda ya gode wa Amirkawa a kan irin taimakon da suka yi wa jama'a, ya kuma kafa wata doka ta shugaban ƙasa, don ma'aikatan gwamnatin tarayya su inganta harkokin aikin sa-kai.

Ya ziyarci gidan marasa galihu na New Orleans, wanda ma'aikatan sa-kai na Kungiyar Katolika ke gyara.

"Ya ci gaba da cewa na yi matuƙar gode wa dukan masu aikin sa-kai, a kan yadda suke kyautata zamantakewar rayuwar jama'a".

Shugaban ya sungumi wata guduma, ya shiga cikin 'yan aikin sa-kai, a Kauyen Makaɗa na New Orleans, don sake matsuguni ga makaɗa da mawaƙan da suka rasa muhalli.

Ya kuma ya da zango a Cibiyar 'Yan Fito Farin Kaya da ke Biloxi da ke yankin Mississippi, wadda ya kira "cibiyar marayu", inda "wata lalura ta haɗa jama'a wuri guda, domin jama'a su nuna wa maƙwabtansu ƙauna".

Wannan kuma shi ne karo na 11 da shugaban ya kai ziyara a bakin tekun, tun lokacin da guguwar Katrina ta tabka ɓarna a yankin, a ƙarshen watan Agusta.

Wannan ziyarar ta shugaba tana cikin hidimomin mako guda don yin godiya game da irin gudunmawar da masu aikin sa-kai miliyan 65 suka yi, ya kuma roƙi jama'ar Amirka da su taimaka a kan bukatun maƙwabtansu. ■



Shugaba Bush tare da 'yan aikin sakai da bala'in guguwar ruwan Katrina ya abka wa a birnin New Orleans na ƙasar Amirka.

# Nijeriya Ta Samu Agaji Don Magance Illar Tsirrai Domin Taimaka Wa Noman Fadama

Daga
Jim Fisher-Thompson,
Birnin Washington



Gonar Fadama

Bankin Duniya, tare da haɗin gwiwar Cibiyar Harkokin Kyautata Muhalli na Duniya (GEF) da ke Birnin Washington, sun amince da su taimaka wa jama'ar Nijeriya wajen magance illolin tsirran fadamu.

A wata sanarwar da aka bayar ranar 11 ga watan Afrilu, Bankin Duniya ya bayyana tsoma bakinsa ga Rukuni na Biyu na Aikin Bunƙasa Noman Fadamu na Kasa, dangane da magance illolin da tsirrai ke samu a ruwa. Cibiyar Harkokin Kyautata Muhalli ta Duniya (GEF) za ta kuma bayar da gudunmawar dalar Amirka miliyan goma.

Mafi yawan fadamun da ke kusa da koguna sukan malale a lokacin damina. Suna da muhimmanci ga harkokin kiwo da noma da kuma yalwar itatuwa da furanni iri-iri da ke janyo hankalin tsuntsaye na duniya.

Nijeriya na da sassan fadamu har takwas. Sun haɗa da hukumomin noman ranin da ke Sakkwato da Kogin Cadi da Tsakiyar Kogin Neja da Kogin Binuwai da Kudu maso Tsakiya da kuma na Koramun Karƙashin Kasa.

A cewar Bankin na Duniya, talauci na "neman yin katutu" a Nijeriya. Don haka noman rani a fadamu, zai taimaka wajen rage talauci da magance irin illolin da tsirrai ke samu a fadamu da zaizayar ƙasa da kuma gurɓacewar ruwa.

Asali ma, aikin fadamun zai inganta yawan albarkar noman da ake samu a ƙasa da jihohi da ƙananan hukumomi da ƙungiyoyin jama'a, ya kuma yi silar rayar da gandun daji da yankunan da fadamun suke, da kuma tsabtace ruwa na sha da na noma, kamar yadda sanarwar ta bayyana.

Haɗin gwiwar Bankin Duniyar da Kungiyar GEF, zai bayar da kuɗin raya fadamu shida cikin 18 da ke jihohin Nijeriya, ana kuma sa ran mutane dubu 400 za su amfana, in ji Shugaban Ayyukan na Bankin Duniya, Mista Simeon Ehui.

KUNGIYAR KULA DA MUHALLI TA DUNIYA

A 1991 aka kafa Kungiyar GEF, da nufin bai wa ƙasashe masu tasowa taimakon kuɗin inganta muhalli da samar da aikin yi ga jama'a. Har ila yau, don mayar da hankali ga gurɓacewar itatuwa da ruwa da kuma ƙasar noma. Ta kuma duƙufa ga magance kwararowar Hamada da gurɓacewar yanayi.

Masana harkokin kawo ci gaba na Bankin Duniya, tare da Kungiyar GEF, na shirin haɗa gwiwar aiwatarwa da duba gudanar da ayyuka. Tun 1991 bakin yake aiwatar da ayyukan da suka cinye dalar Amirka biliyan 1,972, da Kungiyar GEF ke bayarwa. Bankin, tare da haɗin gwiwar Kungiyar GEF sun ƙiyasta kashe dalar Amirka biliyan 3,037 a ƙasashe 80.

Kungiyar GEF za ta shirya taron masu bai wa gwamnatoci shawarwari damasana harkokin muhalli da kuma sauran jama'a daga ƙasashe 176, a Birnin Cape Town da ke Afirka ta Kudu, a ranakun 29 da 30 na watan Agusta.

Taron zai ɓullo da "manufofin ci gaba da ayyukan Kungiyar GEF da kai ziyara a wuraren da Kungiyar ta GEF ke bayar da kuɗaɗen gudanar da ayyuka", a cewar bayanin yanar-gizon GEF. Domin ƙarin bayani game da Taimakon Amirka ga Afirka, tuntuɓi yanar-gizo ta *Trade and Economic Development.*

■

# An Buɗe Cibiyar Amirka A Bauci

Jakadan Kasar Amirka, a Nijeriya, John Campbell, ya kai ziyarar kwanaki uku zuwa Bauci, a Arewacin Nijeriya, domin saduwa da Gwamnan Jihar Bauci, Alhaji Ahmadu Adamu Mu'azu, ya kuma ƙaddamar da Shirin Musayar Shirye-shirye na Amirka, kazalika da buɗe Cibiyar Amirka, a Cibiyar Nazari ta Iya Abubakar. Shirin na Amirka ya bayar da kyautar kekunan ɗinki 130 da kayayyakin koyarwa 900, ga ƙungiyoyin jama'ar da ba su da galihu, a Jihar Bauci. Jakada Campbell kuma ya duba Cibiyar Kiwon Lafiya ta Yelwa ya kuma bayar da kyaututtuka ga mata da iyalansu, waɗanda suka nuna bajinta ga harkokin iyalai da kula da ƙananan yara. Da ma Hukumar Raya Kasashen waje ta Amirka (USAID) ce, tare da Kungiyar COMPASS suka bayar da kuɗin yi

Duba Shafi Na 16



Gwamna Ahmadu Adamu Mu'azu ne yake yankan ƙyallen duɗe cibiyar Amirka a Bauci tare da Jakadan Amirka John Campbell da wasu jami'an Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja Mista Henry Mendelsohn ( a hagu) da kuma Misis Elizabeth Akinbulumo (a dama).

# "Al'umma Ɗaya Makoma Ɗaya": Saƙo Daga Amirka

*Daga Sani Mohammed,*
*Editan Mujallar MAGAMA*

Kungiyoyi masu zaman kansu, kamar 32 da ɗalibai 900 dake Babban Birnin Tarayya da jihohin Kogi da Nassarawa ne, suka karɓi kyaututtukan kekunan ɗinki da kayayyakin koyarwa, don zama wani ɓangare na Shirin Gwamnatin Amirka Na Tallafa Wa Marasa Galihu. Wannan shirin wani haɗin gwiwa ne tsakanin Ofishin Jakadancin Amirka dake Abuja da kuma Cibiyar Bunƙasa Harkokin Mata ta Ƙasa (NCWD).

Tun kafin a fara rarraba kyautar kayayyakin shirin, an shirya tarurrukan ƙarawa juna ilimi, na matasa da ƙungiyoyi masu zaman kansu (NGOs). Wani shaihin Shirin Fulbright na Amirka, Dokta Emeka Okoli ne, ya yi jagorancin tarurrukan. Ya ɗauki tsawon lokaci yana tantaunawa da ɗalibai game da al'amurran da suka shafi fuskantar ƙalubala da muhimmancin ilimi. Yayinda wata ƙwararren kuma ta kasance da maza da mata, don tantaunawa game da yadda ake ƙwarewa akan dabarun ɗinki.



Wasu daga cikin ɗaliban makarantun sakndare da suka ci gajiyar wannan shiri a lokacin da suke karɓar tasu kyautar.

Mataimakiyar Direktar Harkokin Mata, Misis Olayinka Olatunji, wadda ta wakilci Ministar Harkokin Mata, Hajiya Inna Maryam Ciroma, a wajen rarraba kayayyakin aikin, a Abuja, ranar 11 ga watan Mayun 2006, ta bayyana cewa: "Shirin na Amirka zai kawo ci gba da ƙarfafa hanyoyin bunƙasa tattalin arzikin mata da matasa, kazalika ya inganta samun abin masarufi da yi masu jagoran gano hanyoyin kuɓuta daga talauci".

Ita ma Shugabar Majalisar Gudanarwar Kungiyar ta NCWD, Misis Ijeoma Ironini, ta bayyana cewa: "Wannan karimci na jama'ar Amirka zai faranta wa zuciyoyi da dama, musamman mata, da kuma ƙara danƙon zumunci tsakanin jama'ar Nijeriya da jama'ar Amirka".

Kwamishinan Harkokin Mata na Jihar Kogi, Mai girma M.B. Orebiyi da Babban Darektan Cibiyar Bunƙasa Harkokin Mata ta Kasa, Alhaji Abdulmalik Dawuda, da

Duba Shafi Na 16



Dokta Emeka Okoli (a tsakiya) na tattauna al'umrran da suka shafi ilimi da wata ɗaliba (a dama) tare da Daraktan Sashen Watsa Labaru na Cibiyar Bunƙasa Harkokin Mata na ƙasa, Malam Sadeeq Omar (a hagu).

# An “Amince Da Zaman Lafiya” A Darfur

Kungiyar Kasashen Afirka ta cimma warware matsalar yaƙin basasar da ake yi a Darfur, ranar Juma’a, 5 ga watan Mayu 2006, lokacin da wakilin Gwamnatin Sudan, Magthoub el-Khalifa da Kwamandan Sojojin Kwatar ’Yancin Sudan (wadda ita ta fi kowacce girma a Darfur), Minni Minnawi, suka sanya hannu a kan yarjejeniyar zaman lafiya a Abuja.



Shugaban Tawagar Gwamnatin Amirka zuwa wannan taron sulhu, Mista Robert Zoelick (a tsakiya) tare da Dokta Jendayi Fraxer, Mataimakiyar Sakataren Harkokin Wajen Amirka mai kula da Harkokin Afirka (a hagu).



Wakilin Gwamnatin Sudan Magthoub el Khalifa (a dama) tare da Shugaban ƙungiyar sojin ’yantar da Kudancin Sudan, Minni Minnawi a lokacin da yake sa hannu a yarjejeniyar sulhu.

Ita ko ƙaramar rundunar, a ƙarƙashin jagorancin Abdul Wahid, bata sanya hannu ba, amma ta yi alkawarin za ta amince da duk sharuɗɗan da yarjejeniyar ta tanada. Yarjejeniyar ta yi cikakken bayani game da yadda za a raba jama’a da makamai da wargaza sojojin Rundunar Janjaweed da sauran rundunonin ’yan yaƙin sunƙuru da buɗe hanyoyin inganta tattalin arziƙi da haɗe dakarun da jama’ar Darfur wajen gudanar da harkokin siyasa. Muƙaddashin Sakatariyar Amirka, Robert Zoellick, wanda shi ya jagoranci sasantawar da Mataimakiyar Sakatariyar Amirka, mai kula da harkokin Afirka, Jendayi Frazer da Shugaba Olusegun Obasanjo da Kungiyar Kasashen Afirka da masu sasantawa daga Kungiyar Kasashen Turai, suka kai gwauro-da-mari, don ganin an cimma yarjejeniyar. ■

# ’Yancin ’Yan Jaridu

Ba mu da ’yanci” “Kuma me ya sa gwamnati ke ƙuntata wa gidajen watsa labarai masu zaman kansu a Nijeriya?” Waɗannan su ne tambayoyin da ’yan jaridu 45 daga manyan gidajen watsa labarai da ke Abuja suka tambayi Shugaban Hukumar Dokokin Gudanar da Gidajen Watsa Labarai, Dokta Silas Babajiya Yisa da Shugabar Kwamitin Harkokin Watsa Labarai na Majalisar Wakilai ’Yar Majalisa Abike Dabiri da Shugaban Kwamitin Labarai da Gidajen Watsa Labarai na Majalisar Dattijai, Ɗan Majalisar Dattijai Victor Ndoma-Egba, a Sashen Hulɗa da Jama’a, lokacin da Ofishin Jakadancin Amirka ya shirya wata tattaunawa don tunawa da ranar ’Yancin ’yan Jaridun Duniya. ■



Shugaban kwamitin Harkokin Watsa Labarai Abike Dabiri tare da Dokta Silas Yisa, Shugaban Hukumar Kula da Dokokin Gudanar da gidajen Talabijin da Rediyo da kuma sauran manyan mutane da suka gabatar da kasidu a wannan taro.

# Darfur Na Iya “Wartsakewa”, Amma Da Sauran “Rina-A-Kaba”

## Shugaba Bush Ya Yi Korafi Game Da Darfur

*Daga Charles W. Corey,*
*Birnin Washington*

Asakamakon yarjejeniyar zaman lafiyar da aka sanya wa hannu a Abujar Nijeriya, Yaƙin Darfur na Kasar Sudan zai iya “wartsakewa”, amma har yanzu akwai sauran “rina-a-kaba”, in ji Shugaba Bush, a ranar 8 ga watan Mayu, 2006 lokacin da yake fayyace sababbin hanyoyin kai agajin abinci da waɗansu al’amurran gudanarwa, don taimaka wa waɗanda suka jigata a Darfur.

Shugaban ya yi jawabin ne game da Darfur, a Fadar Gwamnatin Amirka, tare da Sakatariyar Gwamnati, Condoleezza Rice da Muƙaddashin Sakatare, Robert B. Zoellick. Shugaba Bush ya ce, Rice za ta yi wa zaman Majalisar Ɗinkin Duniya jawabi, don tattauna agajin tsaro da taimako a Darfur, a kuma yanke hukuncin da zai hanzarta kai sojojin zaman lafiya a Darfur.

Amirka ta miƙa shawarwarin da za su hanzarta shiryawa da taimaka wa dukan al’amarin tsara sabuwar gwamnati daga Sojojin Kungiyar Afirka, har da sojojin zaman lafiya na Majalisar Ɗinkin Duniya da ita kanta majalisar. Shawarwarin sun yi kira da a faɗaɗa ikon da aka bai wa Ofishin Majalisar Ɗinkin Duniya a Sudan (UNMIS), don bayar da goyon bayan yin amfani da sabuwar yarjejeniyar.



Ɗaya daga cikin ’yan gudun hijirar yaƙin Darfur

Ranar 8 ga watan Mayun, a Birnin New York kuma, Jakadan Amirka a Majalisar Ɗinkin Duniya, John Bolton, ya faɗa wa manema labarai cewa, Amirka ta amince waɗannan shawarwari suna da “matuƙar fa’ida, wajen hanzarta kai sojojin zaman lafiya na Majalisar Ɗinkin Duniya, idan aka lura cewa Ofishin Kungiyar Afirka da ke Sudan ya kai maƙura”.”Muna son a hanzarta kai sojojin zaman lafiya na Majalisar Ɗinkin Duniya”, in ji jakadan.

Amirka ta yi murna da yarjejeniyar ta Darfur da aka sanya wa hannu, ranar 5 ga watan Mayu, a Abuja, a tsakanin gwamnatin Sudan da manyan rundunonin ’yan tawaye, da Rundunar Sojojin Kwatar ’Yanci ta Sudan (SLM), da zama wani muhimmin matakin kawo ƙarshen wahalar da jama’ar Darfur ke sha, ta kuma bayar da damar haifar da zaman lafiya da daidaitawar jama’ar ƙasa.

Yarjejeniyar ta tanadi binciken hanyoyin raba jama’a da makamai da wargaza rundunar janjaweed da sauran rundunonin yaƙi da buɗe hanyar inganta tattalin arziƙi da mayar da sojojin cikin rundunar sojan ƙasa, da sakar wa Yankin Darfur marar kafa harkokin siyasa. ■

# Ziyarar Tawagar Cibiyar Kula Da Harkokin Dimokraɗiyya Ta Ƙasa Da Ƙasa

Ambasada John Campbell ya bayyana cewa zaɓuɓɓukan 2007 wata dama ce ta ci gaba da ƙara wa mulkin dimokuraɗiyya ƙarfi a Nijeriya, kazalika da ɗorewar mulkin a Afirka. Ya yi wannan kalamin ne, lokacin da yake karɓar baƙuncin Cibiyar Kula da Mulkin Dimokuraɗiyya ta Duniya, (NDI), wadda ta zo don duba yanayin zaɓen Nijeriya mai zuwa. Ya ce irin zaratan da ke cikin wannan cibiya, babbar alama ce ta mamaye duniya da mulkin dimokuraɗiyya a tsakanin ƙasashen duniya.

Manyan jiga-jigan da suke cikin tawagar sun haɗa da shugaban Botswana a da, *Sir Ketumile Masire,* da Firayi Ministan Kanada a da, *Mai Martaba Joe Clark,* da tsohon shugaban Mauritaniya, *Mai Martaba Karl Auguste Offman,* da tsohon Gwamnan Yankin New Hampshire, *Mai Martaba Jeanne Shaheen,* da Firayi Ministan Kasar Namibiya *Mai Martaba Hage Geingob,* da tsohon Ministan Ayyuka da Gidaje na Kenya, *Mai Martaba Raila Odinga,* da shugaban 'Yan Gwagwarmayar Amirka, *Mista Martin Luther King III,* da Shugaban Cibiyar ta Kula da Mulkin Dimokuraɗiyya, *Mista Kenneth Wollack.*

Maƙasudin wannan ziyara tasu, ita ce don tabbatar da goyon bayan ƙasashen duniya da kuma nuna sha'awar harkokin gudanar da zaɓen mulkin dimokuraɗiyya a Nijeriya da kuma sake bincikar irin shirye-shiryen da aka yi dangane da zaɓuɓɓukan shugaban ƙasa da gwamnoni da 'yan majalisu a 2007. Wakilan sun sadu da jami'an gwamnati da Hukumar Zaɓe Mai Zaman Kanta da jam'iyyun siyasa da 'yan jaridu da sauran jama'a, kazalika da wakilan ƙungiyoyin ƙasashen duniya.



Tawagar Cibiyar Kula Da Harkokin Dimokuraɗiyya Ta Kasa Da Kasa tare da Jakadan Amirka John Campbell (na farko daga dama a layin farko) da kuma Mataimakiyar Daraktan Hukumar USAID a Nijeriya Natalie Freeman (a hagu) a layi na biyu.

Cibiyar ta NDI zaman kanta take yi, kuma tana taimaka wa jama'a a ƙasashen duniya domin gina harsashin ƙungiyoyin mulkin dimokuraɗiyya. Lokacin da suke mayar da martini a kan neman taimako, ƙwararru da masanan da ke cibiyar ta NDI, sun ce suna baiwa jama'a kayayyakin aikin ƙarfafa kafuwar ƙungiyoyin siyasa da kare halaccin zaɓe da ƙara wa jama'a ƙwarin gwiwar shiga ƙungiyoyin da nuna adalci da gaskiya wajen gudanar da ayyukan gwamnati.

Tun cikin 1999, Cibiyar NDI ke gudanar da ayyukan haɓaka gudanar da zaɓuɓɓukan Majalisar Kasa da gwamnatocin jihohi da ƙungiyoyi. ■

# Jawabin Ambasada John Campbell Wajen Karɓar Ziyarar Baƙuncin Cibiyar NDI A Nijeriya

Abin alfahari ne a gare ni, in kasance da ku a cikin wannan mawuyacin halin da Nijeriya ta shiga a tarihinta.Zaɓuɓɓukan 2007 wata dama ce ta ɗorewar ƙakƙarfan mulkin dimokuraɗiyya a Nijeriya, kazalika da kunnowar kan mulkin na dimokuraɗiyya a Afirka. An yi yunƙuri, gwargwadon iko, a cikin 'yan shekarun nan, a ƙasashe, irin su Kasar Benin, wadda kwanan nan ta gudanar da zaɓen da ta fitar da shugaban ƙasa a karo na uku, lami lafiya, tun da aka fara mulkin farar hula, a shekarar1990. A halin yanzu ma ƙasashen Gana da Senegal da Tsibirin Cape Verde da kuma sauran ƙasashe, suna nan maƙale, don ganin yadda Nijeriya za ta zaɓi shugabanninta.

Muddin aka samu galabar gudanar da zaɓuɓɓukan 2007, to dama ta samu ke nan, ga yaɗuwar abin alheri, wajen kawo kwanciyar hankali a yankin da kuma sama wa jama'arsu yanayin kyakkyawar rayuwa. A matsayinta na shugabar ƙasashe, irin abin da ke faruwa a Nijeriya yana da muhimmanci, ba ga 'yan Nijeriya kaɗai ba, har ma ga waɗanda ba 'yan Nijeriya ba. Kuma kamar yadda ziyarar waɗannan mashahuran mutanen ta nuna mana, a yau, abin da ke faruwa a Nijeriya yana da muhimmanci ga dukan ƙasashen duniya.

Har yanzu akwai cikas ga wajen gudanar da zaɓuɓɓukan gaskiya. An tabka maguɗi a zaɓuɓɓukan dimokuraɗiyya biyu da aka yi a Nijeriya, wanda waɗansu suka ce saboda rashin ƙwakƙwaran shiri ne. Amma a bisa ga yadda Nijeriya ke tafiya, ana ɗan samun ci gaban inganta harkokin zaɓe, amma har yanzu akwai sauran rina a kaba, dangane da nasarar gudanar da Zaɓen 2007.

Har yanzu ba a ɓullo da wata sabuwar hanyar zaɓen da za a yi amfani da ita ba. Duk da kuma ana ƙoƙarin sabunta sunayen masu jefa ƙuri'a, a Babban Birnin Tarayya. An ƙiyasta cewa akwai jama'a fiye da miliyan 60 a ƙasar da har yanzu ba a daidaita rajistarsu ba.

Akwai karin magana biyu da suka fassara wannan lamari: Na farko dai *"an makaro wajen ginar rijiya, tun da tuni gida ya kama da wuta"*. Kuma *"dukan kifin da ya san cewa ruwa ya fara ƙafe masa, da wuya a bar shi a baya"*.

Sa'ar kuma ita ce har yanzu gidan bai kama da wuta ba. A bisa irin ƙoƙarin da aka san Nijeriya da shi, har yanzu ba a makara ba, ga magance irin matsalolin da ake samu, wajen shirya gudanar da zaɓuɓɓuka.

Na san kuma, waɗannan baƙin namu, za su iya bayar da shawarwari ga waɗanda aka zaɓa da shugabannin jam'iyyun siyasa da kuma ƙungiyoyin fafitikar nema wa jama'a 'yanci, don taimaka wa abokanmu su guje wa ƙafewar ruwa da inganta darajar Nijeriya, don gudanar da zaɓuɓɓukan adalci a 2007. ■




Zaɓuɓɓukan 2007 su ne babban ƙalubalen da Nijeriya ke fuskanta a idon duniya a yanzu.

*A tuntuɓe mu a yanar gizo: http//nigeria.usembassy.gov/domin karin bayani*

Daga Shafi Na 10
## ...Cibiyar Amirka A Bauci

wa Asibitin Yelwa kwaskwarima.

Gwamna Ahmadu Adamu Mu'azu ya yi wa Ambasada Campbell kyakkyawar tarba, a inda suka ɗaga tutar fara bikin da kuma ƙaddamar da Cibiyar ta Amirka. Gwamna Mu'azu ya zagaya da Jakada Campbell wurare da dama na ayyukan da gwamnatinsa ta yi, ciki kuwa har da Makarantar Gwaji da Asibitin Kwararru. Har ila yau, Ambasada Campbell ya kai ziyarar



Asibitin Yelwa da ƙungiyar COMPASS ta gyara da tallafin Hukumar USAID


Jami'an ƙungiyar COMPASS da na Ofishin Jakadancin Amirka da ƙaramar Hukumar Bauci da suka hallarci taron ba da kyaututtuka ga iyalan da suka nuna bajinta ga harkokin raya ƙananan yara.

ban-girma ga Mai Martaba Sarkin Bauci, kuma Shugaban Majalisar Sarakunan Jihar, Alhaji (Dokta) Suleimanu Adamu, inda ya miƙa gaisuwar ɗaukacin jama'ar Amirka.

Bugu da ƙari, Ambasada Campbell ya sadu da jama'ar Jihar Bauci, waɗanda suka ci gajiyar tallafin zuwa Amirka, don ƙaro ilimi. Ya kuma yi wa manema labarai jawabi, a cibiyar ta Amirka, ya kuma halarci wata liyafar cin abinci da Gwamna Ahmadu Adamu Mu'azu ya shirya masa. ■

Daga Shafi Na 11
## "Al'uma Ɗaya Makoma Ɗaya"


Mista James Moulom, Jami'in Sashen Al'adu na Ofishin Jakadancin Amirka (a hagu) tare da ɗarurruwan ɗalibai da suka hallarci bikin.

shugabannin ƙungiyoyi masu zaman kansu (NGOs) da ɗalibai da manyan ma'aikata daga Hukumar Raya Babban Birnin Tarayya (FCT) da jihohin Kogi da Nassarwa da Shugabar Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka, Misis Shirley Lisenby ne suka halarci wannan gagarumin biki.

Misis Lisenby ta ce "maƙasudin wannan shirin shine don ya fahimtar da jama'a game da Amirka da kuma tunanin jama'ar Amirka game da 'yanci da mulkin dimokuraɗiyya da harkokin kasuwanci da kuma yin haƙuri da juna". Babban burin wannan shirin shine ya inganta halayyar rayuwar jama'ar da ba su da galihu a jihohi 13 na ƙasar nan.

Shirin na Amirka yana gina jama'a ya kuma inganta danƙon zumunci tsakanin jama'ar Amirka da Musulumi da jama'a marasa galihu a duniya. Kayayyakin koyon ilimi dubu 10 da kekenan ɗinki dubu ɗaya da 500 aka bayar ga jama'ar jihohi 12 da aka zaɓo a Nijeriya. Ana kuma koyar da yin amfani da waɗannan kayayyakin, a dukan jihohin da aka bayar da su. ■

# Shirin PEPFAR A Kan Kanjamau A Nijeriya Na Duba Ci Gaban Da Aka Samu



Ministan kiwon Lafiya Farfesa Eyitayo Lambo (a dama) tare da Ambasada John Campbell (a tsakiya) da kuma ƙaramin Minista a ma'aikatan tsaro Dokta Roland Oritsejifor.

Duk da yake akwai mutane dubu takwas da ke mutuwa, kullum, kuma akwai dubu 14 da ke kamuwa da cutar ƙanjamau kullum, har yanzu Shirin Shugaba A kan Bayar Da Agaji, PEPFAR, na samun gagarumar nasara, a Nijeriya, dangane da yaƙar cutar ƙanjamau. Wannan shi ne taken da Jakadan Amirka, John Campbell, ya ɗauka, wajen taron haɗin gwiwar yi wa manema labarai jawabi game da ayyukan Shirin PEPFAR, tare da, Ministan Lafiya Farfesa Eyitayo Lambo da Shugaban Kwamitin Kanjamau na Kasa, Farfesa Babatunde Ositimehin.

Lokacin da yake bayani da hotunan majigi, Babban Jami'in Cibiyar Nazarin Cututtuka da Rigakafinsu, Dokta John Vertefeuille, ya nuna irin nasarorin da Shirin PEPFAR ya samu a Nijeriya, kazalika da bayyana sauran ayyukan shirin, kamar su bayar da maganin da ke inganta garkuwan jikin wanda ya kamu da cutar ƙanjamau (ARV) da allurar rigakafin yaɗuwar cutar daga uwa zuwa jaririnta (PMTC) da tallafa wa yara da marayun da bala'in ya shafa (OVC). Kashi biyar cikin 100 na 'yan Nijeriya, watau mutum miliyan uku da dubu 500 ke ɗauke da cutar ta ƙanjamau, wanda ya sa Nijeriya ta zama ta uku a duniya wajen yawan waɗanda suka kamu da cutar. Waɗanda suka halarci taron, sun haɗa da Karamin Ministan Tsaro, Roland Oritsejifor da Manajan Shirye-shiryen Sashen Tsaro na Ma'aikatar Tsaro, Graham Chadwick.

An ƙaddamar da Shirin PEPFAR ne da dalar Amirka miliyan dubu 15. Kuma Nijeriya na cikin ƙasashe 15 da shirin zai yi wa aiki. Tuni har an kashe dalar Amirka miliyan 198 a 2006, domin faɗaɗa shirin. ■



Masana da jami'an kiwon lafiya da suka hallarci taron

# Jakadan Amirka Ya Kammala Ziyarar Aiki A Kano

Jakadan Amirka a Nijeriya, John Campbell ya kammala ziyarar aiki ta kwanaki biyu zuwa Jihar Kano, a inda ya yi wata lacca game da zaɓe mai zuwa a Nijeriya. A lokacin ziyarar tasa, jakadan ya sadu da Gwamnan Jihar Kano, Malam Ibrahim Shekarau ya kuma kai ziyarar ban girma ga Sarkin Kano, Mai Martaba, Alhaji (Dr) Ado Bayero.

Lokacin da yake jawabi a laccar, a Cibiyar Amirka, Ambasada Campbell ya ce, zaɓen 2007, wata dama ce ga Nijeriya da za ta nuna wa duniya cewa, ga irin matsayinta.

Da yake bayyana irin faɗi-tashin da Amirka ta yi, Ambasada Campbell ya nuna irin muhimmancin da ke tattare da yin rajistar zaɓen 2007. Ya nuna cewa "Ya kamata a yi taka-tsantsan wajen ɗaukar duk wani matakin da ya shafi zaɓen. Babban ginshiƙin al'amarin kuwa shi ne yin rajistar zaɓe". Ya roƙi jama'ar Nijeriya, da su yi amfani da damar da suke da ita, ta yin zaɓe, wajen yin rajista, a lokacin shirin sabunta rajistar masu jefa ƙuri'a, da Hukumar Zaɓe Mai Zaman Kanta za ta yi, a dukan faɗin ƙasa. ■



Ambasada John Campbell a fadar mai martaba Sarkin Kano tare da tawagarsa ta Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.

## Ɓangaren Laccar Ambasada Campbell Game Da Zaɓe

- Ana iya cewa tafarkin dimokuraɗiyya tamkar balaguro ne. A dukan balaguro kuwa, da wuya a ce babu wahala a cikinsa. Wani lokacin a samu gargada, a wani lokacin ma a sha baƙar wahala. Amma idan har aka kamanta yin gaskiya, za a daɗe ana ja, har a kai ga gaci.

- A faɗakar da masu jefa ƙuri'a irin muhimmancin da ke tattare da ƙuri'arsu. Kamar yadda shugaban Amirka na shida, John Quincy Adams da kuma babban ɗan John Adams, shugaban Amirka na biyu suka bayyana: *"A duk lokacin da za ka jefa ƙuri'a ka tuna da aƙidarka, duk da yake ba kai kaɗai za ka jefa ƙuri'a ba, komai daɗin baki, kada ka bari ka yi asarar ƙuri'arka".*

- Wata babbar matsalar da ke damun masu jefa ƙuri'a ita ce rashin wayewar kai. Masu jefa ƙuri'a da dama ba su kulawa da yadda harkokin siyasa ke tafiya, don haka ba su damu da muhimmancin kaɗa ƙuri'a ba.

- Bisa ga irin yadda aka ji jama'ar Amirka sun yi gwagwarmaya, to, za a ga cewa suna tausayawa da kuma taimaka wa ƙoƙarin da Nijeriya ke yi, don inganta



Ambasada Campbell a lokacin da yake gabatar da lacca game da zaɓe a cibiyar Amirka da ke birnin Kano.

harkokin zaɓuɓɓukanta. Dukan nasarar da jama'ar ƙasa za su samu wajen gudanar da zaɓen adalci, a gare mu wata gwagwarmaya ce da aka shafe ƙarni biyu ana nema, kuma muna kan bakanmu har sai an tabbatar da adalci. Amerika na tare da Nijeriya, da dukan wanda ya ɗauki tafarkin dimokuraɗiyya da bin dokoki. Kuma a shirye muke don taimaka wa ƙoƙarin da muke yi, na ganin an gudanar da rajista da harkokin zaɓe.


Ɓangaren al'ulmmar Kano da suka saurari wannan lacca wanda manyan mutane da dama suka halarta.

- Dukan abubuwan da ke faruwa a Nijeriya ba wata matsala ba ce, illa abin da mulkin dimokuraɗiyya ya gada a Afirka. Lokacin da ya kawo ziyara a Nijeriya, a matsayin wakilin Cibiyar Kula Da Mulkin Dimokuraɗiyya Da Gudanar da Zaɓe ta Duniya, tsohon Shugaban Ƙasar Botswana, Sir Ketumile Masire, ya nuna cewa: "Dukan ƙasashen Afirka sun yi wa Nijeriya zurun don ganin abin da za ta yi a 2007. Kuma nasararta ita ce nasarar Afirka".

*A tuntuɓe mu a yanar gizo: http//nigeria.usembassy.gov/domin ƙarin bayani*

Zuwa ga Babban Edita,

Da fatan kai da duk ma'aikatanka kuna cikin ƙoshin lafiya. Allah ya sa haka, Amin. Dalilin wannan wasiƙar shi ne, domin na nemi ka dinga aiko min da wannan mujallar taka – mai matukar farin jini a duk lokacin da aka buga ta. Hakika na karanta wannan mujallar ce a wajen wani abokina, kuma na fahimci cewar tana da matuƙar muhimmanci ƙwarai da gaske.

Da fatan edita zai duba wannan kuka nawa, kuma zai taimaka ya share min hawayena. Zan dakata a nan, da fatan zan ji daga gare ka. Ina yi maka fatan alheri ko da yaushe.

Naka,
Ka'Abu Abubakar Sadiq
Kano

Zuwa ga babban edita,

Bayan dubun gaisuwa irin ta musulunci, yaya ayyuka, ina mai fatan alheri a gare mu duka, amin. Haka kuma ina mai miƙa dubun gaisuwata ga ɗaukacin ma'aikatanku, ina fatan suna cikin ƙoshin lafiya.

Dalilin wannan takarda tawa ita ce in nuna godiyata ga wannan aiki naku da kuke yi, na ilmantar da mutane sha'anin yau da kullum. Haka kuma ina mai miƙa dubun gaisuwata ga daukacin ma'aikatanku. Ina fatan suna cikin ƙoshin lafiya.

Haka kuma kuna wayar mani da kaina dangane da yadda kuke tsakulo labarai da abubuwan da suka shafi rayuwar matasa na yau da kullum.

Daga karshe ina mai fatan za ku dinga aiko mani da wannan mujallar a duk wata don ilmantar da ni game da sha'ani ko wainar da ake toyawa a duniyar nan tamu.

Mai ƙaunarku,
Abdullahi M. Abba Gana
Jalingo.

Zuwa ga Edita,

Ni Mai bukatar karanta jarida ne yadda ya kamata, kuma inda jaridarku ta-ke, ina son ta. Kuma ina jin daɗin karanta ta sosai. Saboda haka, ina son ku rinƙa aiko mani da kowace fitowarta wata-wata.

Kuma ina son ku rinka buga ta kullum kuma ku aika mun ta wannan adireshi da na bayar.

Haruna Bello Jarmai
Kano.

Kuma zaku iya karanta mujallarmu a intanet. Don haka, ku aiko mana da adireshinku na e-mail a wannan adireshi: *magama-ng@lists.state.gov* domin mu rika aiko muku da mujallarmu kai tsaye a duk lokacin da muka fito. ■

## RA'AYINKA

Idan ka samu mujallar *Magama,* muna bukatar ra'ayinka game da ita.
Suna .................................................
.........................................................
Adireshi na e-mail.............................
.........................................................
.........................................................

Za'a iya aiko mana da wasiƙu ta hanyar e-mail a wannan adireshi: magama@state.gov

*Ka aiko mana da dukan bayanai ta hanyar e-mail ko kuma akwatin gidan waya mai lamba: 5760 Garki, Abuja.*

e-mail zuwa ga edita: magama@state.gov

# Ziyarar Ambasada John Campbell Zuwa Bauci



A Fadar Sarkin Bauci, Alhaji (Dr.) Suleimanu Adamu a lokacin da Galadima ke miƙa masa kyautar da sarki ya ba shi



A Maƙabartar marigayi Firayim Minista Abubakar Tafawa Balewa da ke cikin garin Bauci




Tare da Uwargidan Gwamna Hajiya Ashe Mu'azu (a tsakiya) da kwamishiniyar Harkokin Mata na Jihar Bauci Barista Jiddah Mustapha lokacin da suke duba kekunan ɗinki da kuma kayayyakin karatu da ƙasar Amirka ta bada kyautarsu ga al'umman Bauci.



Gwamna Ahmadu Adamu Mu'azu (a hagu) tare da Ambasada John Campbell a lokacin da yake duba ayyukan raya jiha daban-daban da Gwamnan ya yi.



A lokacin da yake yaba ma iyaye da suka raini 'ya'yansu ta hanyar kariya daga cututtuka kamar yadda ƙungiyar Hukumar USAID/COMPASS tare da ma'akatar kiwon lafiya ta Jihar Bauci suka bada shawara ayi a Asibitin Yelwa.



Ambasada Campbell a lokacin da yake miƙa ma Galadiman Bauci kyautar littafi a kan al'adun ƙasar Amirka

# Shirin Amirka Na "Al'umma Ɗaya Makoma Ɗaya"



Lokacin da Shugabanin wannan shiri suke miƙa ma ɗaya daga cikin ƙungiyoyin da suka ci gajiyar kekunan ɗinki a yankunan Birnin Tarayya, da Jihohin Nasarawa da Kogi. Daga hagu akwai: Shirley, Lisenby Jami'ar Sashen Al'adu na Ofishin Jakadancin Amirka da Misis Olayinka Olatunjim Wakiliyar Ministar Harkokin Mata Hajiya inna Maryam Ciroma, Babbar Baƙuwar bikin raba waɗannan kayayyakin kyauta, sai kuma Alhaji Abdulmalik Dawuda, Babban Daraktan Cibiyar Raya Harkokin Mata ta ƙasa.

## Yuni 2006

| Sun | Mon | Tue | Wed | Thu | Fri | Sat |
|---|---|---|---|---|---|---|
| | | Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | | 1 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 2 | 3 |
| 4 | 5 Ranar Bikin ƙulawa da Muhalli ta Duniya | 6 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 7 | 8 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 9 | 10 |
| 11 | 12 | 13 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 14 | 15 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 16 | 17 |
| 18 | 19 | 20 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 21 | 22 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 23 | 24 |
| 25 | 26 | 27 Bayanin da Sashen Hulɗa da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 28 | 29 | 30 | |

Wallafar Ofishin Jakadancin Amirka, Nijeriya